Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
DOI: https://doi.org/10.65760/kassu.i1.37 Website: www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Wasu Ɓoyayyin Taurari a Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi

**Hassan Muhammad**
Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Jihar Sakkwato.

**Corresponding Author: Hassan Muhammad** muhammadhassan6060@gmail.com
07037158242

**Tsakure**

*A adabin baka na Hausawa, waƙa tana ɗaya daga cikin manyan hanyoyin isar da saƙo da hikima. Waƙar baka na da salo da fasaha iri-iri, ciki har da ɓoyayyen saƙo. Ɗaya daga cikin salo mafi ƙayatarwa a waƙoƙin Kassu Zurmi shi ne amfani da ɓoyayyin taurari, wato bayani da yabon mutum ko hali cikin salo na ɓoyewa. Ɓoyayyin taurari a adabi na nufin wasu mutane ko halaye da aka bayyana cikin waƙa ta hanyar nuni ko alama, ba tare da an ambaci sunayen waɗanda suka aikata su kai tsaye ba. Hakan yana buƙatar basira da fahimtar yadda makaɗin ke sarrafa kalmomi cikin tsarin labari amma a sigar waƙa don bayyana su waye ne ɓoyayyin taurari. Wannan nazari da za a gudanar an yi masa suna da 'Wasu |oyayyin taurari a wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi'. Nazarin zai yi tsinkaye ne a wasu waƙoƙin makaɗin tare da fito da wasu ɗiyan waƙoƙi da makaɗin ya yi amfani da su, wanda a cikin su za a bayyana yadda makaɗin ya ambaci ɓoyayyen tauraro. Nazarin zai taƙaita ne ga waƙoƙi biyu na makaɗin, kuma da su ne za a yi ƙoƙarin fito da ƙudurin wannan maƙala. Waƙoƙin su ne 'Waƙar Nomau Namagarya' da 'Waƙar Na Gidan Duwa Maidabo Gajere Mazaizan Duniya'.*

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Wannan takarda ta yi ƙoƙari ne wajen nazarin wasu ɓoyayyin taurari a cikin wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi wanda yake makaɗin maza ne. Wannan nazari zai yi ƙoƙarin fito da wasu ɗiyan waƙoƙi na Kassu Zurmi waɗanda ake ganin makaɗin ya yi amfani da ɓoyayyen tauraro a cikinsu, tare da bayaninsu gwargwadon fahimta. Kafin shiga cikin ƙunshiyar wannan nazari za a fara da taƙaitaccen bayani kan fitilun kalmomi na wannan bincike. Fitilun kalmomin su ne kalmar tauraro da kalmar ɓoyayye. Bayan wannan, sai

bayanin wasu ɓoyayyin taurari da aka ci karo da su a cikin wasu ɗiyan waƙoƙin Kassu Zurmi. Za a rufe wannan bincike da kawo sakamakon abin da nazarin ya gano.

### 1.1 Hanyoyin Tattara Bayanai

A cikin al'amarin bincike kowane iri ne, akwai hanyoyi daban-daban na tattara bayanai, kuma zaɓin hanyar ya danganta ga irin binciken da ake yi, daɗa na kimiyya ne ko zamantakewa ne ko na adabi ne, da dai sauransu. Daga cikin waɗannan hanyoyi akwai tambayoyin waɗanda ake tsarawa a takarda don rarrabawa ga jama'a, akwai hirar fuskantar-juna, akwai kallon halayen jama'a, akwai karanta tushen bayanai da tattara bayanai ta intanet, akwai kuma gwaje-gwaje da sauran hanyoyin bincike makamantan waɗannan. A wannan nazari za a yi ƙoƙarin bin waɗannan hanyoyi da ke tafe:

i. Samo matanin rubutattun waƙoƙin makaɗin don tantance kalmomi da jumlolin da makaɗin ya faɗa.
ii. Binciken kafar sadarwa domin zaƙulo waƙoƙin Kassu Zurmi daga manhajar bidmit (vidmate) da sauraronsu don fito da abin da nazari ke buƙata.
iii. Tattaunawa da masana adabin Hausa daban-daban da kuma waɗanda suka naƙalci waƙoƙin makaɗin kamar Abubakar Sayaya da Abdullahi Birnin Magaji da Ɗanmadamin Birnin Magaji da sauransu da kuma karanta rubuce-rubucen da aka yi a kan makaɗin.

### 1.2 Taƙaitaccen Tarihin Kassu Zurmi

Alhaji Abubakar Kassu Zurmi shi ne cikakken sunansa, an haife shi a garin Magarya da ke cikin ƙasar Zurmi wadda ita Zurmi ƙaramar hukuma ce ta jihar Zamfara. Kassu Zurmi ya zauna ne a Kadawa wanda yake gari ne da nisansa kafin a ƙarasa Magarya tafiyar kilo mita biyu ne. Sunan mahaifin Kassu Zurmi Muhammadu Ganga wanda yake makaɗin farauta ne kuma a wurinsa ne Kassu ya yi gadon kiɗan farauta. Kassu bai yi ilimin zamani ba amma ya ɗan taɓa karatun Alƙur'ani, kuma tun lokacin da ya isa a kira shi da mutum mai hankali ya fara bin mahaifinsa wurin kiɗan farauta (Magaji, 2016:9).

Duk wanda ya san Kassu, ya san shi ne a matsayin makaɗin maza wato dukkan waɗanda yake yi wa kiɗa jarumai ne waɗanda ko a cikin maza lalle sun yi zara wati sai jarumin da zai iya bari a yanke shi ko a sare shi, ko jarumin da zai iya shiga cikin ruƙuƙin daji domin farauta da jarumin da zai iya bin dare ya tafi har wani gari domin ya yo sata. Haka kuma a matsayinsa na makaɗin farauta ba wai gidajensu kawai yake bi idan suna biki ya kama ba, a'a tare da shi ake zuwa dajin farautar (Magaji, 2016:10). A cikin waƙar Gagarau na Magaji cewa ya yi:

> Jagora: Tahiya Madoka ko dajin Kuna,
> Kowaj ji 'yan kalangaina na tahi an nan,
> Sai ɗa da ɗa ka kai naman daji.

Kassu yana da makaɗa guda uku, kowane daga cikin su yana da kalangunsa wanda a koyaushe idan ban da wurin farauta suna tare. Wani muhimmin abu shi ne duk makaɗansa iyakacinsu kiɗan, Kassu ne yake tsara waƙoƙinsa kuma shi kaɗai yake yi, ba a yi masa amshi, don haka Kassu makaɗi ne na kaɗaita wanda yake ƙulla waƙa shi kaɗai, ba tare da an yi masa ƙari ko amshi na gindin waƙa ba (Magaji, 2016:13).

Kassu ya sami ɗaukaka a wajen kiɗan farauta da na tauri, har ma da na ɓarayin wanda hakan ya sa Sarkin Zurmi ya naɗa shi sarkin makaɗan maza na ƙasarsa. Kassu ya yi arziki a kan wannan sana'a ta kiɗa duk ko da yake yana haɗa wa da noma amma kiɗan shi ne a

gaba. Bayan haka Kassu yana da kyakkyawar dangantaka tsakaninsa da sauran makaɗan ƙasar Hausa kamar Alhaji Mamman Shata wanda har biya masa kuɗin jirgi ya yi ya je Makka ya yiwo sallah kamar yadda ya nuna a wani ɗan waƙarsa:

Jagora: Kai ubangidan Shanu da Gambu,
Na Dela albarkacinka nis sabu da Shata,
Hay yay yi man kujerah haji niz zo.

Magaji (2016:10) ya bayyana cewa waƙoƙi biyu ne na 'yan tauri suka fito da Kassu Zurmi sarari har aka san shi, kuma waƙoƙin suna cikin tsofaffin waƙoƙinsa da aka saka a garmaho. Waƙoƙin su ne 'Waƙar Nomau Namagarya da 'Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo. Haka ya sake bayyana cewa kafin rasuwar Kassu Zurmi ya yi fiye da shekaru ashirin bai je farauta ba, a dalilin gwamnati ta hana saboda wasu dalilai wanda daga cikin su akwai yawan rasa rayuka da ake yi in an fita.

## 1.3 Tauraro

Ita wannan kalma ta tauraro tana ɗauke da lamirin namiji, mace kuwa tauraruwa, jam'i kuma taurari ko tauraru (Sa'id, 2006:433). Al'ummar Hausawa suna kallon wannan kalma ta tauraro da ma'anoni daban-daban, na farko dai suna kallonta da wata halitta da ke bayyana a sararin sama da daddare tana haske. Haka ana kallonta da wani shahararren mutum ko wata halitta da ke fitowa a cikin labaru. Haka kuma tana ɗaukar wata alama ta farin gashi a girar doki, ko kuma sa'a da mutum ya samu a wani al'amari da ya sa a gaba (Sa'id, 2006:433).

Masana a fannin adabin zamani musamman a kan abin da ya shafi ƙagaggun labaran Hausa sun faɗi abin da ake nufi da tauraro a nazarin adabin Hausa. Mukhtar (2004:68) ya nuna tauraro shi ne mutumen da mawallafi yakan sako a cikin labarinsa. Ya ƙara da cewa su taurarin cikin labari an kasa su zuwa gida-gida dangane da irin da rawar da kowane ya taka a cikin labari, akwai babban tauraro wanda shi ne aka gina labari a kansa, kuma shi ne wanda mawallafi ke ta faman tattalinsa wanda ba a son wani abu ya same shi a cikin labarin, akwai kuma ƙananan taurari waɗanda ke taimakawa babban tauraro.

A wannan nazari an dubi taurao a matsayin duk wani mutum ko wata halitta da mawallafi ya zaɓa domin ya warware jigon labari ta amfani da wannan mutumin ko wannan halittar.

### 1.3.1 Ire-iren Taurari

Mukhtar (2004:69) ya nuna duk da kasancewar akan sami babban tauraro da ƙanana to bai hana a sami wasu nau'o'in taurari waɗanda akan gane sunayensu ta hanyar yanayinsu ko kuma ta hanyar irin rawar da suka taka a cikin labari. Ya kawo nau'o'in taurari uku a nasa nazarin, akwai miƙaƙƙen tauraro wanda da zaran marubuci ya bayyana halinsa, to da jin sunansa mai karatu ba zai yi mamakin abin da zai aikata ba, akwai kuma tauraro mai gammo wanda shi kuma halayyarsa gagara-koyo ce, wato shi yadda yake idan ya yi wani halin kirki ko na taimako a cikin labari, to wani lokaci kuma sai ya yi abin tsiya yadda za a riƙa mamakin anya kuwa shi ne zai aikata haka, wato shi a taƙaice koyaushe cikin bai wa mai karatu mamaki yake. Haka kuma akwai tauraro mai walƙiya wanda shi kuma mawallafi kan sako cikin labari ba tare da ya gabatar da shi ga mai karatu ba, sannan ya janye shi ba tare da ya sanar da shi ba.

Bunza (2011:14-17) a nazarin da ya gabatar ya nuna akwai ire-iren taurari guda shida, su ne fitaccen tauraro da babban tauraro da ɓoyayyen tauraro da ƙaramin tauraro da

tauraro mai tsawon rai da kuma mai gajeren rai. Ya ci gaba da cewa fitaccen tauraro shi ne tauraron da ya taka muhimmiyar rawa tun daga farko har zuwa ƙarshen labari wanda kuma ta kansa ne ake warware jigon labari. Babban tauraro kuwa, shi ne wanda ya taka muhimmiyar rawa wajen warware jigon labari wato tauraro ne mafi kusanci ga fitaccen tauraro. Ƙaramin tauraro kuwa, shi ne wanda rawar da ya taka a labari ta taimaka wajen isar da saƙon labarin, sannan shi ne wanda mawallafi bai faye damuwa da abin da ya same shi ba a cikin labari. Shi kuma ɓoyayyen tauraro shi ne wanda ba a ambatar sunansa a cikin labari, sai dai a yi amfani da rukunin kalmomin da ake kira da mafayyata a tsarin nahawun Hausa irinsu wani ko wata ko wasu ko waɗansu da sauran kalmomi ire-irensu. Shi kuwa tauraro mai tsawon rai shi ne wanda rawar gani ta tsawon lokaci a cikin labari, wato shi ne wanda mawallafin labari kan raya na tsawon lokaci ana yi da shi, ana kuma jin ɗuriyarsa nan da can, wani lokaci sai a ɓoye shi a sa shi a duhu sai kuma can gaba a ci gaba da shi, wato dai akan ɗauki dogon zango ana warwarar jigon labari tare da shi. Tauraro mai gajeren rai kuwa, shi ne wanda mawallafin labari ya kawo a wani wuri cikin labari, sai kuma ya aje shi alhali labari bai ƙare ba, irin wannan tauraro kan taka rawa ce 'yar kaɗan domin kawai ƙulla zaren wani batu da ba a son ya katse domin katsewarsa na iya zama wani cikas ga warwarar jigon labari.

### 1.4 Kalmar |oye/|oyayye

Kalmar "ɓoyayye" an tsagota ne a ilimin ƙirar kalma (*morphology*) daga ginshiƙin aikatau "ɓoye", wato ɓoye abu. Ga yadda kalmar ta samo asali ɓoyayye = ɓoye + -ayy-e. Kalmar "ɓoye": Aikatau ne (verb) – yana nufin ɓatar da abu ko ɓoye shi daga gani. Kalmar ɓoye na nufin sa abu wurin da ba za a gani ba ko kuma kasancewa a wani wuri don kada wani ya ganka (Sa'id, 2006:65).

### 1.5 |oyayyen Tauraro

Duk da yake a baya an faɗi abin da ake nufi da ɓoyayyen tauraro a binciken da Bunza (2011:14-17) ya gabatar inda ya ce ɓoyayyen tauraro shi ne wanda ba a ambatar sunansa a cikin labari, sai dai a yi amfani da rukunin kalmomin da ake kira da mafayyata a tsarin nahawun Hausa irinsu wani ko wata ko wasu ko waɗansu da sauran kalmomi ire-irensu.

A wannan nazari an kalli ɓoyayyen tauraro a matayin wani mutum mai matuƙar muhimmanci a cikin waƙa ko labari ko wasan kwaikwayo ko wani aiki na adabi, wanda ba a bayyana shi kai tsaye ba, amma dai ana iya gane sa ta ambatar da wani suna wanda ba sunansa na yanka ba, ko kuma a yi amfani da mafayyatan kalmomi na tsarin ilimin nahawu kamar irin wani ko wata ko wasu da sauransu.

### 2.1 |oyayyin Taurari a wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi

Yanzu kuma za a fara kawo ɗiyan waƙar da wannan nazari ya ci karo da su, tare da bayanin yadda ɓoyayyen tauraro ya bayyana a cikin su. Ga su kamar haka:

Jagora: Na tambaya cikin 'yan tauri,
To kuma na tambaya ga manyan makaɗa,
Wa anka ba doki da gangami ba ni ba?
Wane ɗan tauri yay yi doki da gangami garinsu?
A'a, doki da gangami sai Nomau na Magarya,
Don Ubanbalindo shi ya ishe ni hak Kadawa.

Jagora: Yac ce,
Kassu ana biɗak ka da doki,
Ga ka kana alhwarma,
Nac ce,
Ɗankarma ba ni ƙamnaƙ ƙarya,
Wa ka sai mani doki Magarya?
Nomau ne, ko abin tuwo ba ya da shi,
Sai yac ce, "Ai da tarbace za a saye,
Da tarbace za a saye?
Su wa su wa sunka shiga?
Na san dattiɓan Magarya zana mani su,
Cikinsu na san kowa,
Na san mai iya yi.

Jagora: Wai kun ji Kassu doki yaka so,
Dokin wa?
Domin Nomau,
Ah to ya ba shi,
Ah a Saraki ba haka kai ba,
Ai ku nac ce da tarbace za ku saye,
Yac ce lalala babu ruwana,
In don ni ko anini nau ba ya shiga,
Tunda Nomau bai raga ma kowa Magarya,
Sannan wani ba ya sa shi aiki ya tahi.
(Waƙar Nomau Namagarya)

Ɗiyan waƙar na nuni da wata tambaya da binciken da mai waƙa ke yi game da shahararren jarumi ko ɗan tauri wanda ya cancanci kyautar doki da gangami alamar karɓuwa da ɗaukaka a al'adar tauri. An tabbatar da cewa Nomau Namagarya ne kaɗai ya cancanci wannan ɗaukaka da kuma Ubanbalindo, wanda shi ne ya ishe shi hak Kadawa. Ɓoyayyen tauraro a nan shi ne 'Ubanbalindo', dalili kuwa, shi ne ba a bayyana shi kai tsaye ba. Makaɗin ya fara tambaya da damuwa, yana buƙatar sanin wanene ya cancanci girmamawa, ba tare da faɗin sunan Ubanbalindo nan da nan ba. A ƙarshe ne kawai aka ambace shi, bayan an bayyana cewa ba kowa ne ya cancanta ba, sai aka ce "Don Ubanbalindo shi ya ishe ni hak Kadawa." Wannan na nuna cewa shi ne tauraron da aka ɓoye tun farko, amma yana da matuƙar tasiri a waƙar. Haka kuma ana iya fahimtar cewa shi ne jigon waƙar, amma aka zo da shi ta salo mai nuni da girmamawa da sirri, wanda yake da ƙima a cikin adabin waƙar Hausa. Wasu ɓoyayyin taurari da suka sake bayyana a ɗiyan waƙar su ne Ɗankarma da kuma Saraki, Ɗankarma shi ne wanda Nomau ya ce ƙarya yake masa don yana ganin kamar isgilanci yake masa don ya ce za a saya masa doki a magarya ga ya ko ba ya shiri da kowa. Shi kuma Saraki cewa ya yi lalle za a iya saya masa doki amma sai da tarbace. A taƙaice Ubanbalindo da Ɗankarma da Saraki su ne ɓoyayyin taurari da aka gano a ɗiyan waƙar da ke sama.
A wasu ɗiyan waƙar ga abin da ake cewa:
Jagora: Na Audu jikan Jatau,
Baba jigon hwaɗa karen masu gari,
Kasko ba horon karnai,
Audu lahani mai tada ciniki ba a saye,
Kanƙandandi maganin masu kwaɗo,

Doki na bar zuwa ba ka yi shi ba,
Yaz zo yac ce Saraki,
Ka ga shi doki sabadda shi za ni hwashi,
Shegen dai ya shige gida ya ƙi hita,
Ya ce ya bar zuwa gida ban yi shi ba.

Ɗiyan waƙar da ke sama suna bayani ne a kan Audu jikan Jatau tun daga kan ɗan waƙa na farko har zuwa na biyar wato kamar kirari ake masa ana koɗa shi, amma shi wannan nazari akalarsa ta karkata ne a kan ɓoyayyin taurari, wannan ne ya sa ba za a mayar da hankali wajen sharhin koɗawar da ake yi wa Audu jikan Jatau ba. |oyayyen tauraro a ɗiyan waƙar shi ne Saraki wanda shi ne aka zo aka gaya masa cewa za a yi fashi ne saboda doki. Abin da ya sa ya zama ɓoyayyen tauraro, shi ne ba a bayyana ko waye shi ba illa kawai an nuna yadda aka yi masa magana.

Jagora: Sannan ɗebo wuta ga ragga ka hita,
Ba dai mai gini Magarya sai na rihewa,
To koma daz zuwa gidan Ɗan'aljanna busa 'yabbura'uba,
Sai daji Namagarya rantsuwakka ta kasan,
Zama tare da 'yan gudummawa za ni hita,
Wuta nah his san,
Bila'i na wuta.

Su kuma waɗannan ɗiyan waƙar ɓoyayyen tauraron da ke cikin su, shi ne Ɗan'aljanna wanda shi ma ba a bayyana ko waye shi ba illa kawai an nuna a je gidansa a busa wuta kuma ba bayyana dalilin haka ba, sai dai an nuna ƙyamar zama da masu neman gudummuwa da kuma bala'in da ke cikin wuta. Amma shi wannan Ɗan'aljanna a hirar da aka yi da Ɗanmadamin Birnin Magaji ranar Talata 16/04/2025 ya ce Ɗan'aljanna ne ke da gida a farkon shiga garin Magarya amma Kassu Zurmi ya ba Nomau shawara da ya cinnawa gidan wuta domin ta zama gobarar da za ta sanya Kassu fita tare da masu kashe wutar a matsayin dalilin ficewarsa daga Magarya saboda rantsuwar da ya yi cewa idan ba a ba shi doki ba, ba zai fita ba.

Jagora: Yac ce,
Kassu shawarakka ita za ni biya,
Baba in kau ka bi ta gobe dokin aka yi,
Magarya ko ba a da shi,
Sai ga Nomau ana ta gyaran kulki da kambuna za a hwashi,
Aha,
Da Allah yat tashi taimakonmu da dokin swahiya ta waye,
Tun da yas sa buda ba ka ganin tahin hannunka,
Iska kau yas sumƙaƙo ba ka jin taƙauye Magarya,
Sai nij ji gangami rariya-rariya,
Kun jiya Kadirawa jama'am Magarya,
Abin da Saraki yac ce a hwaɗa muku,
Kowa ya dibi gidanai,
In an ga sanwa wuri a kashe,
Ta ɗaka kau a sa makarai da yawa,
Allah ya raba mu da iskan ga lahiya,
Don Allah Saraki zaburo za ya hita,
Yara ashe Saraki ba ya taƙama,

Ya ga abin da za ya hwaɗa ma gari,
Dole ya'i sai nig ga Saraki an hito ba rawani,
Tun jiya na hwaɗi ku kame mani shi,
Yas sa haɓe sun ka kame mashi shi.

A waɗannan ɗiyan waƙa an nuna irin saƙon Saraki da aka iyar ga jama'ar gari, na su yi hattara da tashin wuta saboda bala'in da ke tattare da ita. A nan kamar yana nuni ne da cewa Saraki kamar shi ne shugaba a cikin garin Magarya don an nuna ba ya da taƙama ya hito ba rawani, amma ba a fito fili ƙarara aka nuna waye shi ba, kuma wannan dalilin ne ya sa shi Sarakin ya zama ɓoyayyen tauraro a cikin ɗiyan waƙar.

A wasu ɗiyan waƙa na wata waƙar ga abin da Kassu ke cewa:
Jagora: Na gode na Gidan Duwa,
Gajere mazaizan duniya,
Tauri ba ƙarya ba ne,
Tauri ya kyauta mai duniya,
Kuma ya kyauta mai lahira,
Yanzu wani ya ce ƙarya nikai,
Za ni hwaɗa muku abin da yak kyauta mai lahira,
Bari yac can masassarar annoba tam matsa,
Da anka yi yayin kwallara,
Ta wullaƙ ƙatta ɗai takai,
Ka ji wani ƙato can ya mutu. x2
(Waƙar Na Gidan Duwa Maidabo Gajere Mazaizan Duniya)

A cikin ɗiyan waƙar akwai magana ta godiya ga wani ko wani wuri da aka samu gata ko kuma wanda ya bayar da taimako. "Gidan Duwa" na iya nufin wani gida ko sansani da ke da alaƙa da wani jarumi ko shahararre. Haka an nuna akwai wani mutum mai gajeren tsawo amma cike da ƙwazo da ƙarfin hali. Kalmar "mazaizan" na nufin jarumai ko masu kishi da jajircewa. Hakan na nuna cewa duk da cewa yana da jiki gajere, amma jarumtarsa ta ninka girman sa. Wannan na nuna irin tauraro da ba kowa ya lura da shi ba wato ɓoyayye. Haka an nuna gaskiyar halin "tauri" wato jarunta ko ƙarfin hali, kuma ana fuskantar ƙalubale daga masu ƙarya, amma dai an tabbatar da cewa wannan hali na tauri na gaske ne, ba ƙage ba, sannan ita jarunta ko ƙarfin hali na tauri yana kawo lada da daraja a duniya da lahira, don wasu na ganin tauri a matsayin wani hali mai kyau da za a yi koyi da shi. Haka a cikin ɗiyan waƙar an bayyana wani aiki ko hali na jarumi wanda ba kawai yana da amfani a duniya ba, har ma yana da lada da falala a lahira. Haka an nuna wani mutum da ya tafi kai tsaye zuwa wurin da annoba ko wata babbar cuta ke yaɗuwa. Wannan babban alamar jarumta ce. a al'ada, mutane sukan guji irin waɗannan wurare saboda fargaba da tsoro, amma wannan jarumi ya matsa alamar sadaukarwa da rashin jin tsoron mutuwa domin ceto wasu. Kalmar "kwallara" (cholera) na nuna wata cuta mai saurin yaɗuwa da kashe mutane. Ana nuni da wani yanayi na bala'i da fargaba. A wannan lokaci ne ɓoyayyen taurarorn ya nuna bajintarsa, ya tsaya tsayin daka, ya je inda ba kowa zai iya zuwa ba. Kuma an nuna irin saurin yaɗuwar cutar ko bala'in kamar wuta ce da ta wulla ƙatta (wani babban gida ko yanki). Sai dai "ɗai takai" na iya nufin wani mutum guda kacal ne ya tunkari wannan bala'i, wanda ke nuni da ɓoyayyen tauraro da ke aiki ba tare da tayin jama'a ba. A taƙaice dai a ɗiyan waƙar da aka yi wannan bayani a kansu sun nuna kalmar wani da ta maimaitu sau biyu ita ke nuni da ɓoyayyin taurari.

Jama'a kun ji kiɗin na Gidan Duwa
Wani ɓaga mai taurin ido
Anna kun san Maidabo?
Wani ya san Maidabo
Wani ko bai sani ba suna nai ɗai yaj jiya,

Shina nan wani mai haɓa gajera mai ɗan mummuƙe,
Shina na Gidan Duwa
Na koma ta Gidan Duwa,
Inda gajere mazaizan duniya,
Albarkacin karenka kakan ga karen wani,
Daure Maidabo saboda kai nis sauka Gidan Duwa.
(Waƙar Na Gidan Duwa Maidabo Gajere Mazaizan Duniya)

A waɗannan ɗiyan waƙa da ke sama da ke nuni da wani ɓaga mai taurin ido da kuma wani ya san mai dabo wani ko bai sani ba, suna kawai ya ji duk suna nuni da ɓoyayyin taurari. Abin da ke nuni da haka ita ce mafayyaciyar kalma da aka iya amfani da ita a ɗiyan waƙar, wato ita ce kalmar **wani** wadda ta maimaitu sau biyar a ɗiyan waƙar kuma duk mabambantan taurari ne ba tauraro ɗaya ake nufi ba.

**3.1 Wasu Muhimman Abubuwan Lura a Nazarin**

Akwai wasu muhimman abubuwa da ya kamata a lura da su a wannan nazarin kasancewar nazari ne da aka gabatar a kan waƙar baka, amma sai dai abin da aka nazarta an fi nazarinsa a rubutun zube musamman a ƙagaggun labarai ko wasan kwaikwayo. Dalilin haka ne ya kamata a lura da hikima da salon da ke cikin waƙoƙin Kassu Zurmi waɗanda suka sa aka yi nazarin ɓoyayyin taurari a wasu daga cikin waƙoƙinsa. Abubuwan su ne:

i. Amfani da salo na ɓoye gaskiya tare buɗe ƙofofin fahimtar sirrin waƙoƙinsa.
ii. Siffanta wani jarumi ko shugaba ko hali mai kyau ko akasin haka cikin sirri tare da nuna basira da fasaha ta hanyar zayyana tauraron da ba a bayyana kai tsaye ba.
iii. Taimaka wa masu karatu su fahimci yadda mawaƙin ke sadarwa ga jama'a ba tare da faɗin sunan mutum ba, tare da ƙarfafa amfani da tunani mai zurfi wajen saurаron Waƙoƙinsa.

**1.1 Sakamakon Bincike**

A ƙarshen wannan nazari da aka gudanar an gano wasu 'yan hikimomi da ke ƙunshe ga ɓoye taurari musamman irin wannan ɓangare na adabi da ya shafi waƙar baka. Abin da aka gano shi ne:

i. A wasu lokuta makaɗi kan yi amfani da dabarar ɓoye suna ko hali na mutum ko wani abu a cikin waƙa, ba don komai ba, sai don kawai kariyar kai daga zargi ko gardama.
ii. Haka an gano akwai ƙima ƙwarai da gaske da fasaha a waƙa a dalilin ɓoye sunan abu ko halayyarsa.

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

iii. A wani lokaci ba komi ke haifar da wannan hikima ba to ɓoyo suna ko hali illa fasahar ƙirƙira da sha'awa da kuma kewayawar maganganu a cikin ɗiyan waƙa.

## 1.0 Kammalawa

Wannan nazari kamar yadda aka gani an gudanar da shi ne a kan abin da ya shafi wasu ɓoyayyin taurari a cikin wasu waƙoƙin Makaɗa Kassu Zurmi. Nazarin ya kalli waƙoƙi biyu na makaɗin inda ya fito da ɓoyayyin taurari a ciki. |oyayyin taurarin da nazarin ya ci karo da sun haɗa da Ɗankarma da Ubanbalindo da Ɗan'aljanna da Saraki da sauransu. Kafin nan nazarin ya yi ƙoƙarin bayyana waye tauraro da ire-irensa da kuma waye ɓoyayyen taurao. A ƙarshen nazarin an kawo muhimmancin ɓoye tauraro a waƙar baka da ma sauran rukunnan adabin Hausa tare da kawo sakamakon da bincike ya gano.

**Manazarta**


Bunza, H. M. (2012). Tauraro a cikin Kagaggun Labaran Hausa: Nazari daga Littafin *Jiki Magayi*. Kundin Digiri na Ɗaya. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Funtua, A. I. (2015). Nazari a kan Waƙoƙin Makaɗan Baka na Hausa a Jihar Katsina Daga 1978 Zuwa 2012. Kundin Digiri na Uku (Ph.D Thesis) . Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Ɗangambo, A. (1984). *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Kano: Maɗaba'ar Kamfanin 'Triumph' Gidan Sa'adu Zungur.

Gusau, S. M. (1988). Waƙoƙin Makaɗan fada: Sigoginsu da Yanaye-yanayensu. Kundin Digiri na uku (Ph. D Thesis). Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Gusau, S. M. (1995, 2003). *Jagoran Nazarin Waƙar Baka.* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Magaji, A. (2016). Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa. Ibadan: Specrum Books Limited.

Mukhtar, I. (2004). *Jagoran Nazarin Kagaggun Labarai. Tsari na Uku.* Kano: Iya Ruwa Publishers.

Sa'id, B. (2006). *Kamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.